# DAMAKWARADIYYA

## DA MATSAYINTA

## A MAHANGAR

# MUSULUNCI

**NA**

**DR. YAHAYA TANKO**

## Bayani Daga Mawallafi:

Duk wanda yake son ya ƙara buga wannan littafi, ko wani kashi daga cikinsa ko ya fassara shi zuwa wani harshen, to akwai buƙatar neman rubutaccen izini daga mawallafin.

An fara bugawa, a watan al-Muharram, shekarar 1442 H, daidai da watan Satumba. na shekarar 2020 M.

ISBN: 978-978-984-812-6

## Abubuwan Da Suke Ciki:


Gabatarwa…………………………………………………………………......................................1

Ma'anar Siyasa ……………………………………………………………………………6

Ma'anar Siyasa A Musulunci ……………………………………………………………...6

Asalin Siyasar Turai ………………………………………………………………………10

Asalin Siyasar Musulunci…………………………………………………………………..10

Ma'anar Damakwarađiyya…………………………………………………………………13

Shin Damakwarađiyya Musulunci ce?...................................................................................15

Fa'idojin Damakwarađiyya…………………………………………………………………16

Wuraren Da Ake zaton Damakwarađiyya Ta Yi Kama Da Musulunci ……………………………..17

Aibukan Damakwarađiyya Guda Ashirin Da đaya (21) A Mahangar Musulunci ………………..23

Tana Bai Wa đan 'adam Haƙƙin kafa doka……………………………………………………23

Tana Bai Wa Shugabanni Haƙƙin Allah……………………………………………………….37

Tana Raba Kan Musulmi…………………………………………………………………42

Farar Da Ƙiyayya Da Gaba………………………………………………………………….44

Tana Sa Yin Alƙawuran ƙarya...................................……………………………………...47

Tana Sa Bayar Da Rashawa ..........................................................................................................48

Jam'iyyar Da Ta Yi Nasara Tana komawa kamar Sarautar Gado.........................................................53

Tana Fifita Yawa A Kan Nagarta.................................................................................................54

Tana Sa Karkata Ga Ayyukan Raya Ƙasa…......................................................................................59

Tana Đaukar Mutane Kowa Da Kowa Da Kowa Bai Đaya................................................................63

Yin Amfani Da Tasirin Kafofin Yađa Labarai.................................................................................67

Biyan Wasu Kuđađe Kafin Zama Đan Takara..................................................................................68

Ɓarnar Kuđin Jama'a......................................................................................................................69

Saba'in Cikin Đari Na 'Yan Najeriya Ba Sa Yin Zaɓe.......................................................................70

Zaɓe Ya Kan Nuna Jam'iyyar Da Ta Fi Yawan Ƙuri'a, Amma Mafi Yawan Jama'a Ba Sa Son Ta...72

Tana Sa Aci Zaɓe Da Ƙasa da Kashi Hamsin Cikin Ɗari.....73

Tana Sawa A Zaɓi Shugaba Domin Ya Bayar Da Cin Hanci.....74

Tana Samar Da Shugabanni Maƙaryata.....76

Mace Za Ta Iya Zama Shugaba.....78

Naɗa Mutane A Muƙaman Da Basu Da Ƙwarewa Akai.....80

Tana Janyo Rashin Ɗorewar Ayyuka.....83

Nasiha Ga 'Yan uwa Musulmi.....85

Kammalawa.....88

# GABATARWA

Godiya ta tabbata ga Allah. Muna godiya gare shi. Muna neman taimakonsa. Muna neman gafararsa. Muna neman tsarinsa daga sharrin kawunanmu, da munanan ayyukanmu. Wanda Allah ya shirye shi, shi ne zai nemi shiriya. Wanda kuwa ya ɓatar da shi babu mai shiryar da shi. Na shaida babu abin bauta wa sai Allah, shi kadai. Na kuma shaida Annabi Muhammad (Sallallahu Alaihi Wasallam) bawansa ne, kuma Manzonsa ne. Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Bayan haka, yana da kyau mu sani cewa, asalin wannan rubutu maƙabalace wadda na gabatar a wurare daban-daban, gabanin zaɓen da aka gudanar a Najeriya na shekarar 2019, domin wayar da kan yan 'uwa Musulmi Su san mace ce Damakwaraɗiyya.

Mu sani cewa, babbar matsalarmu mu Musulmi ita ce, mafi yawanmu ba mu ma san ma'anar addini ba. Wajibi ne mu sani cewa, abin da ake nufi da addini shi ne, **tsarin rayuwa wanda Allah Mahalicci ya shimfiɗa wa bayinsa domin su tafiyar da rayuwarsu a kai.** Ba kamar yadda mafi yawanmu muke dunƙule shi a cikin Salla Azumi zuwa Haji, karatun Al-Ƙur'ani da zikiri ba. Dalilina a nan shi ne, yayin da Allah ya kammala saukar da al-Kur'ani, cewa ya yi ya kammala mana addininmu a gare mu.

Idan kuwa haka ne, to ai sai mu ga cewa Al-Ƙur'ani ba kawai Salla, Azumi, zuwa. Haji, karatun Al-Ƙur'ani da zikiri kawai ya ƙunsa ba. Abin da yake cikin Al-Ƙur'ani rayuwa ce baki ɗaya. Su waɗan can abubuwan ana kiran su. Arkanul Islami watau rukunan Musulunci. Ko a kira su Sha'a'irul Islami, watau futattun alamomin Musulunci.

A taƙaice dai mun san cewa a kan kasa fannonin rayuwa zuwa kashi shida: Fannin aƙida da bayyanannun ayyukan ibada (kamar Salla Azumi....) Fannin Ilimi da tarbiya. Fannin zamantakewa. Fannin Tattalin arziki. Fannin siyasa da fanni Shari'ah. A dukkanin waɗan nan fannoni na rayuwa babu wanda Allah bai shinfiɗa mana nasa tsarin ba, da yadda za mu gudanar da shi, wanda ya kira shi da sunan addini. Ke nan muna ƙara nanatawa cewa, ma'anar addini shi ne tsarin rayuwa wanda Mahalicci ya shinfiɗa mana ya kuma wajabta mana bin sa.

Don haka mu sani cewa idan muka bi wani tsarin, wanda ba nasa ba, ba za mu taɓa ganin daidai ba. Mu sani cewa idan muka bar tsarin Allah muka bi tsarin da wasu suka tsara mana to mun mayar da kanmu bayin waɗan nan mutanen. Su muke bauta wa Allah ba . Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:

*Ko suna da wasu waɗanda suka yi tarayya da su da Allah, waɗanda Suka tsara musu addini (hanyar rayuwa) wadda Allah bai halatta musu ba?" (suratus shura, aya ta:21).*

Wannan ne ya sanya nake son a wannan haɗuwar tamu mu tattauna a kan ɗaya daga cikin abubuwan nan shida, watau mu ɗauki Siyasa (Damakwaraɗiyya) ta zama jigo, saboda ita muke ciki a yanzu. Domin haka nake son matashiyarmu ta zamo kamar haka: Damakwaraɗiyya Da Matsayinta A Mahangar Musulunci. Wataƙila ma fahimci shin ta dace da tsarin Allah kokuwa. Allah ya taimake mu amin.

**Dr. Yahaya Tanko 08060846703**

# MA'ANAR SIYASA:

Siyasa kalma ce ta larabci, watau ‘As- Siyasah”, ma'anarta 1ta ce tafiyar da shugabancin jama a. Haka nan Larabawa suna amfaní da kalmar a sanda suke nufin shugabanci mai shiryarwa. Watau ba wanda zai kai waɗanda ake shugabantar ga rashin nasara ko halaka ko ɓata ba.

### Ma'anar Siyasa A Musulunci:

Ibnu Khaldun ya fassara siyasa a tafarkin Musulunci da cewa, ita ce ɗora kafatanin al'uma a kan mahangar Shari'ar Musulunci, ga abin da yake maslaha ne a gare su (watau abinda zai zama mai amfani a gare su) a lahirarsu; da ma na duniyarsu, wanda amfanin zai koma ga ita lahirar. Tunda dai su al'amuran duniya gaba ɗayansu, a wajen Allah, maslahar Su tana komawa ne ga lahira. (lta siyasar Musulunci) a haƙiƙaninta halifanci ce na mai kafa dokoki (watau Allah), game da kare addini da tafiyar da Siyasar duniya da shi.

Amma malamai sukan ƙara bayani cewa, shugaba zai iya aiwatar da abinda yake maslaha ne, ko da kuwa bai zo ƙuru-ƙuru a cikin Al-Ƙur'ani da Sunna ba. Matuƙar dai bai saɓa wa shi Al-Ƙur'anin ko Sunnar ba.

Abul Wafa'i Ibnu Aƙil ya ce: Siyasa,ita ce aikin da zai sa mutane su fi kusanta abin da yake shi ne daidai, da nisantar ɓarna, koda kuwa Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) bai shar'anta shi ba, kuma wahayi bai saukar da shi ba (Ya ce): "Idan faɗinka cewa, babu siyasa sai abin da ya dace da Shari' ah, kana nufin abin da bai saɓa wa abinda shari'ah ta ce ba, to maganarka ta yi daidai

Idan har mutum ya fahimci ma’anar siyasa a Musulunci; kamar yadda malamai suka yi bayaninta; zai gane cewa babu bam banci tsakanin addini da siyasa. Siyasa ɓangare ne na addini. Domin shi addini hanyar rayuwa ne gaba ɗaya. Haka kuma mutum zai fahimci cewa siyasa tana da alaƙa da lahira. Ba harka ce ta duniya kaƙai ba.

## ASALIN SIYASAR TURAI:

Game da bayanin asalin siyasar Turai, dole sai an taɓo malamin palsafar nan na Greek, watau Aplaɗun “plato”, wanda ya rubuta littafi mai suna jumhuriya “Republic”, a shekarar 375 BC (watau kafin haihuwar Annabi isa Alaihissalam). Da ɗalibinsa mai suna Arasɗo “Aristotle” wanda ya rubuta littafi mai suna As siyasah “the politics” a tsakanin shekara ta 335 da shekara ta 323 BC, (lokacinsa da ya rubuta mafi yawan Littafansa). A cikinsa ne ya yi bincike game da tsarin zamantakewar ɗan ‘adam, tun daga zamantakewar iyali, zuwa zaman gari guda, zuwa na ƙasa da talakawa da dangantakar ita ƙasashen.

## Asalin Siyasar Musulunci:

Ita kuwa siyasar Musulunci ta faro ne tun daga kan Annabi Adamu (Alaihissalam). Shi ne shugaba na farko, wanda ya wakilci Allah a bayan ƙasa[4]. Sai sauran manzanni, kamar Annabi Nuhu, Annabi Dawud, Annabi lbrahim, Annabi Musa, Annabi Isa da Manzonmu Annabi Muhammad (Sallallahu Alaihi Wasallam) Allah (Subahanahu Wata’ala) yana cewa:

*"Hakika Allah ya zaɓi Annabi Adamu da Annabi Nuhu da iyalin Annabi ibrahim da iyalin Imrana (ya fifita su) a kan sauran halitta( Suratu Ali Imrana, aya ta : 33)*

Abin nufi a nan shi ne, dukkanin manzanni Allah yana aiko su ne domin su tafiyar da tsarin rayuwar al'umominsu kamar yadda Allah yake so. Kowanne annabi za mu ga ba kawai Salla da Zakka da Azumi yake koya wa mutanensa ba. Misali, za mu ga wani yana umarni da cika ma' auni (kamar annabi Shu'aibu),.Wani yana hana luwaɗi da fashi da makami (kamar annabi Luɗu). Wani yana ƙoƙarin tsamo wani jinsi daga bautarwar wani jinsin (kamar annabi Musa). Wani ya yi mulkin da babu irinsa (kamar annabi Sulaimanu). Ga kuma annabi Yusufa, wanda ya riƙe wani ɓangare na harkar mulkin ƙasar Masar, da sauransu. Ashe ke nan, asalin siyasar Musulunci gaba yake da na Turai. Ya fi shi daɗewa. Ya fi shi ta wajen kyan asali. Domin shi daga Allah yake.

## MA'ANAR DAMAKWARAƊIYYA:

Abin da ake nufi da damakwaraɗiyya shi ne, jama'a su mulki kansu da kansu. Saɓanin mulkin sarauta (Monarchy). Saɓanin mulkin wasu zaɓaɓɓun mutane (Aristocracy). Saɓanin mulkin mutane da sunan addini, wanda ake nuna kamar Allah ne yake tafiyar da lamarin, (Theocracy ). Watau mulkar mutane ta hanyar fakewa da cewa Allah ne yake mulkarsu.

An ƙago damakwaraɗiyya ne a ƙarni na shida kafin haihuwar Annabi Isa (Alaihissalam), a garin Asina "Athens na ƙasar Girik.

Domin a kauce wa duk waɗancan hanyoyin mulkin da muka ambata.

Damakwaraɗiyya iri uku ce: Akwai mulkin damakwaraɗiyya na kai tsaye, direct democracy. Shi ne wanda mutane za su haɗu gaba ɗaya su tsara wa kansu dokokin da za su tafiyar da rayuwarsu a kai. Akwai mulkin damakwaraɗiyya mai kama da na kaitsaye (semi-democracy) shine wanda wakilan da aka zaɓa zasu dinga tafiyar da gwamnati, amma talakawa su ne suke zaɓar abin da suke son a yi musu. Akwai kuma mulkin damakwaraɗiyya na wakilci (representatives democracy). Shi kuma shine wanda wakilan da aka zaɓa za su dinga tafiyar da gwamnati, da suffar wakilai na waɗanda suka zaɓe su. Ba sai sun dawo sun tambaye su abinda suke so ba.

Ya kamata mu lura cewa, a duk waɗannan nau'o i guda uku mutane su ne suke kafa wa kansu dokoki. Babu inda aka yi maganar Allah. Wan nan shi ya sa suke yi wa mulkin damakwaraɗiyya kirari kamar haka: **"Government of the people by the people for the people"**

Watau mutane su ne masu tsara wa kansu dokokin da za su tafiyar da rayuwarsu a kai, kuma su aiwatar da su a kan sauran jama'ar da suke mulka.

## Shin Damakwaraɗiyya Musulunci Ce?

Da yawa daga cikin mutane sun ɗauka cewa ma'anar damakwaraɗiyya shi ne tabbatar da adalci a tsakanin jama'a, da daidaito da tabbatar da jin daɗin rayuwa. To, wataƙila a wasu lokuta wasu su ga kamar hakan. Amma wannan ba zai sa a ce damakwaraɗiyya Musulunci ce ba.

## Fa'idojin Damakwaraɗiyya:

Abin da aka fi zayyanawa daga cikin fa'idoji /amfanin damakwaraɗiyya su ne:

a) Bai wa mutane dama su zaɓi wanda suke son ya mulke su.

b) Wai tana hana yin babakere a mulki.

c) Wai tana tabbatar da daidaito a tsakanin jama'a, a zamantakewa da tattalin arziki da siyasa da walwala.

d) Wai tana sa shugabanni su yi wa jama'a aiki, kasancewar su suka zaɓe Su.

e) Takan sa talakawa su dinga jin ana yin mulki da su, tun daga gudanar da zaɓe da kuma jan su a jiki da masu mulkin za su dinga yi, domin su taimaka musu, da sauransu[6].

## Wuraren Da Ake Zaton Damakwaraɗiyya ta yi kama da musulunci:

Akwai wurare uku a cikin damakwaraɗiyya waɗanda suka sa wasu suke kamanta ta da Musulunci, amma a haƙiƙanin lamari sun sha bamban.

1. **Majalisun Dokoki Ba Shura Ba Ne:**

A siyasar Musulunci akwai abinda ake kira Majalisar shura wadda wasu suke daidaita tada majalisar dokoki. To a gaskiyar lamari ita Damakwaraɗiyya babu tsarin Shura a cikinta, (Democracy is NOT Shura). Saboda:

a) A tsarin Shura ba a tattauna abin da Allah ya yanke hukunci a kansa.

b) A tsarin Shura shawarar da majalisa ta yanke ba ta zama dole ga shugaba ya yi aiki da ita. Domin Shawara aka ba shi. Ba doka ba.

c) A tsarin Shura ana naɗa mutane ne masu suffofi kamar haka: (i) Musulmi

(ii) Masu cikakken hankali (iii) Masu ilimin addini (iv) Ko masu ƙwarewa a wata harka ta rayuwa (v) Masu kyawawan halaye. Watau su zamo adalai ba fasiƙai ba.

2. **Jefa Kuri''a Ba Mubaya'a Ba Ne:** A siyasar Musulunci akwai abinda ake kira mubaya'a, shi ne bayan nagartattun mutane sun zaɓi shugaba sai sauran mutane su dinga zuwa suna nuna yardarsu gare shi. Don haka Jefa ƙuri'a ba daidai yake da "mubayaa ba, ta fuskoki kamar haka:

a) A zaɓen jefa ƙuri'a mutum fiye da ɗaya ne suke tsayawa. Ita kuwa mubaya'a shugaba ake yi wa, bayan an zaɓe shi.

b) Shi zaɓe hanya ce ta ɗarewa muƙamai daban-daban. Ita kuwa mubaya'a sai shugaban al'uma gaba ɗaya ake yi wa.

c) Shi zaɓen jefa ƙuri'a na kowa da kowa ne, ita kuwa nagartattu ake neman su yi, ba kowa da kowa ba. Sai sun yi, san nan sauran jama'a su yi mubaya'a.

d) A tsarin jefa ƙuri'a mutum fiye da ɓaya suna iya cin zaɓe. Ita kuwa ‘mubaya' a da ma mutum ɗaya ake yi wa

Yadda mutane fiye da ɗaya za su ci zaɓe da ƙuri'a ɗaya a tsarin damakwarɗdiyya shi ne, a zaɓen 'yan majalisar dattijai a Najeriya, kowa ƙuri'a ɗaya zai jefa, amma a zaɓi dukkanin yan majalisar dattijai da ita.

3. **Yancin Damakwaraɗiyya Ba Yanci Ba Ne:**Damakwaraɗiyya tana bai wa ɗan'adam ‘yanci na ƙarya, mai mummunar manufa (Wrong Meaning in the Use of Freedom).

A Musulunci akwai ‘yanci. Mutum yana da 'yancin ya rayu. Yana da ‘yancin a kare masa dukiyarsa. Yana da ‘yancin a kare masa mutincinsa, da sauransu. Amma shi ‘yancin damakwaraɗiyya manufarsa, a mafi yawan lokuta shi ne, nuna wa ɗan'adam yana da yancin ya saɓa wa dokokin Allah (Subahanahu Wata’ala). Misali:

**Yancin tunani**. Watau mutum zai iya zaɓar tunani wanda zai bauta wa, komai ƙasƙancinsa. Koda kuwa kare ne ko jaki ko ƙabarin wani, kai ko da najasar wani ya zaɓi ya bauta wa, za a ba shi wannan ‘yancin.

**Yancin zaɓin dokar da mutane suka ga dama.** Za su iya cewa, ba za a yanke hannun ɓarawo ba. Zina ba laifi ba ce, sai in ta zama fyaɗe. Auren jinsi halal ne, da sauransu.

Mu sani cewa tunanin ɗan'dam yana da iyaka. Ba zai gano masa komai da Komai ba. Allah (SubahanahuWata’ala) yana nuna mana cewa ‘yancinmu yana da iyaka. Don haka kada mu wuce dokokin Allah. Inda yake cewa:

"Waɗannan dokokin Allah ne, kada ku ƙetare su. Wanda duk ya ƙetare iyakokin Allah waɗannan su ne azzalumai (Suratul Baƙarah, aya ta: 229). Watau sun zalunci kansu. Kuma idan muka duba za mu ga a can inda damakwaraɗiyyar ta fito, 'yancin ba a sake yake ba a wajen su. Misali:

- Mutum ba zai yi tusa a cikin jama'a ba, saboda da'awar ‘yanci. Ba su yarda yana da wannan 'yancin ba.
- Mutum bai isa ya tuƙa abin hawansa ta inda wasu suke tawowa ba, domin taƙamar 'yanci. Da yake ita wannan dokarsu ce, ba ta Allah ba. Kuma sun gane za su cutu.
- Mutum bai isa ya yi gini a gidansa ba tare da ya nemi izini ba, idan aka tambaye shi ya ce yana da 'yanci.
- Duk da cewa mace tana da 'yancin ta sa kayan da take so, waɗanda suka saɓa wa dokokin Allah, amma ba ta isa ta sa kayan yin wanka a bakin ruwa, ta je gidan makoki da su ba.

Ashe ke nan ma'anar yancin shi ne a saɓa wa dokokin Allah. Auren mace fiye da ɗaya haramun ne, amma yin zina da mace fiye da ɗaya halal ne. Yin fyaɗe haramun ne, amma yın zina da mace ko guda nawa ce ya halatta, in dai da yardarta. Da sauransu.

## AIBUKAN DAMAKWARAƊIYYA GUDA ASHIRIN DA ƊAYA (21) A MAHANGAR MUSULUNCI

Mu sani cewa, aibukan da suke cikin damakwaraɗiyya suna da yawa a mahangar Musulunci, fiye da amfanin da ake ruɗarmu da su. Ga muhimmai daga cikin aibukan nata kamar haka:

1. **Tana Bai wa ɗan'adam haƙƙin kafa doka**. (Sovereignty belongs to the People) A musulunci Allah kaɗai Shi ne mai kafa dokoki. Allah Shi ne mai bayar da umarni da hani, da halattawa da haramtawa a dukkanin tsarin rayuwa. Ga wasu ayoyi daga Alƙur'ani da suke tabbatar da haka:

*Haƙiƙa ubangijinku shi ne Allah, Wanda ya halicci sammai da ƙasa, a cikin kwana shida. sannan ya daidaita a Al'arshi: yana rufe yini da dare (shi daren) yana nemansa (shi yinin) ciki hanzari. Da rana da wata da taurari ababen horewa ne da umarminsa. Ku sani cewa, Shi ne mai halitta (don haka) umarmi nasa ne (halacci ko haramci Allah ya ɗaukaka, ubangijin halittu (Suratul A araf, aya ta: 54).*

Wannan aya tana nuna mana cewa, kasancewar Allah shi ya halicci dukkanin halittu na cikin duniyar nan tamu, kuma shi yake sarrafa su, ya zamo wajıbi mu gane, kuma mu yarda, cewa shi kaɗai ya cancanci ya bayar da umarni da hani, da kafa dokoki. Na tabbata cewa lafiyayyen tunani zai yarda cewa, akwai zalunci a ce, ga wanda ya yi halitta kuma yake sarrafa ta, amma wani can ko wasu, su zama su ne masu kafa wa wan nan halittar dokoki da ba su umarni da hani. Allah ya sa mu gane.

***Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce:***

***Kuma ba ya yin tarayya da wani a cikin hukuncinsa da wani a cikin hukuncmsa (Suratul Kahaf, aya ta: 26)***

Malam ibnul jarir yace: "Allah (SubahanahuWata'ala) ba ya sanya wani, in ba shi ba cikin kaddarawarsa da hukuncinsa a Kan halittarsa. Shi kaɗai yake, a cikin hukuncinsa da ƙaddarawarsa a cikin lamnarinsu. haka nan a cikin tsara al 'amuransu da sarrafa su, yadda ya ga dama, kuma yadda ya so

Shi kuma malam Muhammadul Amin Ash Shanƙiiɗi cewa ya yi: "Ma'anar Wannan aya shi ne: Allah, ya girma ya ɗaukaka, ba ya tarayya da wani, a cikin hukuncinsa. Bar wannan Hukunci, nasa ne, shi kaɗai, ya girma ya ɗaukaka. Babu hukunci ga waninsa ko ƙanƙani. Halal shi ne abin da ya halatta. Haram, shi ne abin da ya haramta, maɗaukakin sarki. Abin daya tsara shi ne Addini (watau hanyar rayuwa). Abin da ya yanke shi ne hukunci"

***Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce***

*Shin akwai wani hukunci ban da na Allah? Yayi umarni kada ku bauta wa kowa sai Shi. Wannan shi ne addini (watau tsarin rayuwa) miƙaƙƙe. Amma mafi yawan mutane ba su sani ba'" (Suratu Yusufa, aya ta: 40).*

Wannan yana nuna cewa yin biyayya ga dokar wanin Allah, wadda ta saɓa wa ta Allah, bauta ne ga shi wanda ya kafa wannan dokar. Ko waɗanda suka kafa ta Malam Muhammad Mutawlli ash Sha'araawi a tafsirinsa, ya fassara: da cewa:

“Kada ku bi wani umarni ko hani, sai abinda Allah ya saukar a tsarinsa ma shiryarwa zuwa ga abinda yake daidai, kuma alhairi (ga bayinsa).

Ya fassara

Haƙiƙa wannan shi ne tsari miƙaƙƙe, ba waninsa ba. Amma mafi yawan mutane ba su sani ba, cewa manzanni Sun isar musu da wannan tsarin. Saidai cewa su ba su aiwatar da wannan ilimin ba a ayyukansu.

**Allah (Subahanahu Wata’ala) ya ce:**

Kuma kada ku dinga cewa: wannan halal ne, wannan haram ne, ga abin da harasanku suke suffatawa na ƙarya kuna ƙagar ƙarya ga Allah. Haƙiƙa waɗanda suke ƙagar ƙarya ga Allah ba za su rabauta ba. ɗan jin daɗin ne kaɗan kuma azaba mai raɗaɗi ta tabbata a kansu. (Suratun Nahli, aya ta: l16-117). Wannan ayar tana nuna cewa, waɗanda suke kafa dokoki na halattawa da haramtawa ƙarya suke yi wa Allah.

A nan sai mu duba girman zunubin wanda ya yi wa wani ƙarya. To ina ga wanda ya yi wa Allah ƙarya!

**Allah (Subahanahu Wata’ala) ya ce:**

"Ya kai wannan Annabi, don me za ka dinga haramta wa kanka abin da Allah ya halatta maka, kana neman yardar matanka. (Suratut Tahrimi, aya ta: 1)

Wannan aya tana nuna cewa, ba ma maganar wani ko wasu su kafa wa wasu doka ta haramta musu wani abu ake yi ba, shi kansa mutum ya haramta wa kansa cin wani nau'i na abinci haramun ne. Domin ai ba shi ya yi kansa ba. Wanda ya yi shi shi ne mai wannan haƙƙin.

Kuma sai ayar ta yi mana wani abu mai kama da abin da Bahaushe yake cewa, a tauna tsakuwa domin aya ta ji tsoro. Watau sai aka hana Annabi yin haka. Watau idan wani dalili ya sa mutum ba zai ci wani nau'i na abinci ba, ko ya ji ba ya sha'awarsa sai kawai ya ce ba ya ci. Domin ba shi da ikon kafa wa kansa doka, ta haramta wa kansa wannan abincin.

**Allah (Subahanahu Wata’ala) ya ce:**

*“Idan kuka yi jayayya a kan wani abu, to ku mayar da shi ga Allah da Manzo. Idan kun kasance kun yi imani da Allah da ranar lahira. Wannan shi ya fi alhairi, kuma shi ne abinda ƙarshensa ya fi zama alheri (Suratun Nisa'i, aya ta : 59).*

Wannan ayar tana koyar da mu Musulmi cewa, yayın da wata matsala ta faru a tsakanin al'uma, muke son mu yi maganinta, ba haɗuwa za mu yi mu kafa wa mutane doka ba. A'a, da farko dubawa za mu yi a Al'Ƙur'ani da Hadisan Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam), mu samo mata mafita.

Idan ba mu samu amsa, bayyananniya ba, to sai mu duba mu ga ko ra’ayin magabata na ƙwarai ya haɗu a kan amsa guda ɗaya; Idan ba mu samu ba, to a sannan sai mu yi amfani da tunaninmu, mu aiwatar

da abin da muke ganin ya fi kusa da abin da Allah yake so. Ba wai abin da mu muke so, ko abin da mutanen ƙasa suke so ba.

**Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce:**

"Na rantse da ubangijinka! Ba za su yi imani ba, sai sun hukunta ka a saɓanin da ya faru a tsakaninsu. Sannan ya zamo ba su sami wani ƙunci ba a zukatansu, game da hukuncin da ka yi. Ya zama sun yi cikakkiyar miƙa wuya. (Suratun Nisa i, aya ta: 65).

Ita kuma wannan ayar nuna mana take yi cewa, babu imani ga duk wanda bai hukunta tsarin da Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) zamo da shi, ya zama shi ne hukuncin da ya zaɓa ba Kuma idan aka yi masa hukunci da shi, ya ji babu wata damuwa game da shi. Sai Hadisi

"Daga Adiyyu bin Hatim (Radiyallahu Anhu) ya ce: "Naje wajen Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam), alhali akwai "cross na zinariya a wuyana. Sai ya ce "Ya 'Adiyyu! Cire wannan gunkin daga wuyanka Sai na ji shi yana karanta Suratu Bara 'ah (kamar haka): "Sun riƙi malamansu da masu bautarsu iyayen giji. maimakon Allah Sai na ce: Ya Ma 'aikin Allah! Ba su kasance suna bauta musu ba. Sai ya ce: "Haka ne, amma ai suna halatta musu abin da Allah ya haramta, sai su karɓi halatta warsu. Suna kuma haramta musu abin da Allah ya halatta, sai su karɓi haramcin su. Wannan ita ce bautar da suke yi musu (Tirmizi da Baihaƙi suka ruwaito).

Ya zo a cikin al Mu' jamul Kabir cewa Hatimu ya ce: Sai na ce: Ba mu kasance muna bauta musu ba. Sai ya ce: "Shin ba sa haramta muku abin da Allah ya halatta, sai ku haramta shi. Kuma halatta muku abin da Allah ya haramta sai ku halatta? Sai na ce: Eh, (muna yi) Sai ya ce: "To ai wannan ita ce bautar da kuke yi musu.

Wannan Hadisin yana nuna mana cewa duk sanda wasu za su dinga kafa wa mutane dokokin da suka saɓa da na Allah, su kuma mutanen suna bin su, to bauta musu suke yi. Sun zama su ne allolinsu, maimakon Allah. Kokuma sun haɗa su da Allah a matsayin su ma alloli ne. Watau suna layi ɗaya da Allah, a ɗa'ar da suke yi wa Allah.

2. **Tana Bai wa shugabanni haƙƙin Allah**: (Allah's right given to leaders)

Damakwaraɗiyya tana sa talakawa dogaro ga shugabanni, maimakon Allah. Abin da yake janyo wannan shi ne, a tsarin damakwaraɗiyya shugabanni ne suke yi wa talakawa alƙawuran abin da za su yi musu idan suka zaɓe su. A tsarin siyasar Musulunci babu irin waɗannan alƙawuran. Alƙawarin da shugaba zai ɗauka shi ne, ya tafiyar da talakawansa a kan tsarin littafin Allah da sunnar Manzonsa (Sallallahu Alaihi Wasallam) Shi kuwa wannan tsarin cike yake da adalci da dukkanin jin daɗi na duniya da na lahira. Domin Allah ya fi kowa son bayinsa da tausayin su. Haka nan Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam).

Mu sani cewa, yana daga cikin rukunan Imani, Musulmi ya yarda cewa, abu mai dadi da marar daɗi duka daga Allah suke. Duk da dai cewa shi marar daɗi ɗan' adam ne yake sabbaba shi.

To amma sai gashi damakwaraɗiyya ta sa Musulmi sun mayar da lmaninsu na samun jin daɗi ko shan wuya kacokan, a hannun shugabanni. Maganganun da mutane suke yi suna nuna cewa, yunwa da ƙoshi, daga shugabanni suke zuwa. Su suke janyo arziki da talauci. Walwala da ƙunci, shugabanni ne suke farar da Su Abin nufi a nan shi ne, za ka ga mutane suna ɗora duk wadannan abubuwan a kan jam'iyyar da take mulki, ko shugaban da yake mulki, ba Allah ba.

A tsarin siyasar Musulunci duk wani jin daɗin ɗan'adam Allah ya tsara shi a Al-Ƙur'ani da sunnah. Na taɓa jin wani babban ɗan siyasa a wannan ƙasar tamu (Najeriya), yana yin wata magana kamar haka: Yana cewa PDP ce ta mayar da shi minister. lta ta mayar da shi gwamna.

Don haka idan ka ga bai zama shugaban ƙasa ba. to Allah ne bai ba shi ba. Ka ga a nan jahilci ya sa shi ya danganta jin daɗi da nasara ga PDP, rashin jin daɗi kuwa da faɗuwar zaɓe daga Allah ne

Wannan yana da matuƙar haɗari. Domin ya shafi Imani da ƙaddara. Abu mai daɗi daga Allah ne, sai bawa ya godewa Allah. Marar daɗi ma daga Allah ne amma ɗan'adam ne yake sabbaba shi. Ko kuma Allah ne ya jarrabe shi. Sai bawa ya koma ga Allah ya gyara kurakuransa. Kuma ya yarda cewa, Allah ya san rashin ba shi wannan abin shi ya fi alhairi a gare shi, shi ya sa bai ba shi ba.

Abin nufi dai a nan shi ne, mu sani cewa Allah yana da ta cewa, kuma yana da ruwa da tsaki a tafiyar da harkokinmu. Idan muka saɓa wa tsarinsa, to komai daɗewa, kuma ko da mun ga kyan lamarin da muka tsara wa kanmu da farko, to za mu gamu da taɓarɓarewar Al'amura daga baya. Allah (SubahanahuWata’ala) yana cewa:

“Idan da mutanen gari (ko ƙasa) za su yi imani, su ji tsoron Allah, da mun buɗȇ musu albarkatu daga sama da ƙasa Amma sun ƙaryata, Sai muka riƙe su da abin da suka kasance suna aikatawa" (Suratul A araf, aya ta: 96).

**Allah (Subahanahu Wata’ala) ya ce:**

“Allah ya buga misali da wani gari, wanda yake cikin aminci,cikin nutsuwa, arzikinsu mai yawa, yana zuwar musu daga ko na. Sai Suka kafirce wa ni’imomin Allah Sai Allah ya ɗanɗana musu tufafin yinwa da tsoro, sabo da abin da suke aikatawa (Suratun Nahli, aya ta:112)

Wannan yana nuna mana cewa, rashin bin Allah a tsarin tattalin arzikinmu da zamantakewarmu shi yake sawa komai namu yake taɓarɓarewa. Kuma mu kasa gano bakin zaren. Allah ya sa mu gane.

**Kuma Allah (Subahanahu Wata’ala) ya ce:**

“Kuma duk abin da ya same ku na musiba, to a dalilin abin da hannayenku suka aikata ne. Kuma (Allah) yana yin afuwa kan abubuwa masu yawa (Suratus Shura, aya ta: 30).

**Kuma dai Allah (Subahanahu Wata’ala) yana cewa:**

“Abin da ya same ka Kyakkyawa daga Allah ne. Amma abinda ya same ka mummuna, (to asalinsa) daga gare ka ne” (Suraun Nisa , aya ta: 79).

3. **Tana Raba kan al'umar Musulmi:** (Muslim Nation becomes divided)

A tsarin damakwaraɗiyya, ɗan ƙasarka shi ne ɗan'uwanka, wanda kuke al'uma ɗaya. A musulunci kuwa, Musulmi, a ko'ina yake, shi ne ɗan'uwanka, wanda kuke al'uma ɗaya. Don haka lallai ne kada Musulmi ya so wanda ba Musulmi ba, so har zuci. Kada kuma ya haɗa kai da wanda ba Musulmi ba a cuci. Musulmi. Lallai ne mu kula da wannan.

Domin yana da matukar haɗari. Haɗuwa a jam’iyya daban, haɗuwar addini daban

Kada mu fifita haɗuwar jam’iyya a kan dangantakar mu ta ‘yan uwantakar Musulunci. Allah (Subahanahu Wata’ala) yana cewa:

"Ya ku waɗanda suka yi imani! Kada ku riƙi Yahudu da Nasara abokai mataimaka juna.Sashinsu da sashi  abokan juna ne. **Wanda duk ya riƙe su abokai daga cikinku**, to yana cikinsu. Allah ba ya shiryar da mutanen da suke azzalumai (Suratul Ma 'idah, aya ta: 51)

Abin nufí a nan shi ne, kada mu yarda a cusa mana son ƙasa, ta yadda za mu daidaita Musulmi da wanda ba Musulmi ba. Kada ka yarda ka ƙaunaci Yahudu ko Kirista, balle har ma ta kai ka ga taimaka masa a kan Musulmi. Musulmi shi ne ɗan’uwanka. Shi kuwa wancan yana da nasa ɗan ‘uwan, wanda suke addini ɗaya.Don me za ka tafi cikinsu ka ɗakko ɗan‘uwa , ka bar ‘yan ‘uwanka. Ai ka ƙara musu yawa ke nan. Saboda haka ka zama nasu.

4. **Tana Farar da ƙiyayya da gaba da tashin hankula a tsakanin Musulmi:**

( It Promotes enmity and Violence)

Damakwaraɗiyya tana farar da gaba tsakanin Musulmi. Wannan yana faruwa ne saboda raba kawunan Musulmi jam 'iyyu. Wannan gaba takan kai har ga ɗaukar makamai da kisan juna. Ka ga ke nan, maimakon Allah ya umarce mu mu yaƙi kafirai, domin yaɗa tsarinsa a bayan Kasa (watau addinin Musulunci), mun ƙiyi, sai damakwaraɗiyya ta umarce mu da mu yaƙi Junanmu, muke ta bin umarninta. Allah ya sa mu gane.

Allah (Subahanahu Wata’ala) ya ce:

“Ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗayanku. Kada ku rarraba” (Suratu Ali Imrana, aya ta:103).

**Allah (Subahanahu Wata’ala) ya ce:**

*"Wanda duk ya kashe mumini da gangan, to sakamakonsa wutar Jahannama. Zai dawwama a cikinta. Kuma Allah ya yi fishi da shi. Ya la 'ance shi. Ya tanadar masa azaba mai girma (Suratun Nisa’i, aya ta: 93)*

*Daga lbnu Umar (Radiyallahu Anhu) ya ce: “Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam)  ya ce : ”Mumini ba zai gushe ba cikin yalwa (ta samun gafara) a cikin addininsa, matuƙar bai zubar da jinni haramtacce ba (Bukhari ne uwarto)*

*Daga Barra’u bin Azib, Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "A ce duniya babu ita, ya fi sauƙi a wajen Allah, da a ce an kashe ran Mumini ba da haƙƙi ba (lbnu Majah yaruwaito)*

5. **Tana Sa Yin Alƙawura, har ma da na ƙarya**: (False Promises & Lies)

Wannan addinin namu ya wajabta mana cewa, idan mutum ya yi alƙawari lallai ya cika. Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce: *"Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku dinga cika alƙawura na mu'amaloli (Suratul Ma idah, aya ta: 1).*

Haka nan addininmu ya koyar. da mu cewa, maƙaryaci babban munafiki ne. Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce:

"Alamar munafiki uku ce: "Idan ya yi zance ya yi ƙarya. Idan ya yi alƙawari, ya saɓa. Idan aka amince masa, ya yi ha'inchi" (Bukhari da muslim suka ruwaito).

6. **Tana Sa Bayar da Rashawa Da Yin Ƙage A Yayin Zaɓe (Bribery & ) Blackmailing**

Rashawa ita ce abin da a ke bai wa ma'aikacin gwamnati, na kuɗi ko wani abin, domin ya yi abin da bai halatta ba, ko ya ƙi yin abin da yake shi ne wajibi a mas'alar da take gabansa.

*Daga Abu Hurairah (Radiyallahu Anhu) ya ce: "Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya tsine wa mai cin rashawa da mai bayar da ita a hukunci" (Tirmizi ne ya ruwaito).*

*Daga Abdullahi bin Amr (Radiyallahu Anhu) ya ce: "Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Allah ya tsine wa mai cin rashawa da mai bayar da Ita" (Tirmizi da waninsa suka uwaito).*

A Najeriya ana kiran wannan ɗabi'a da sunan, **cin hanci da rashawa**. Wan nan ya haɗa abin da muka faɗa a sama, da ma duk wata hanya ta satar dukiyar jama'a Mu sani cewa, a Musulunci satar dukiyar gwamnati babban laifi ne.

**Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce:**

*Wanda duk ya ɗauki dukiyar jama'a a ɓoye (watau dukiyar gwamnati zai zo da abin da ya ɗauka ranar ƙiyama "(Suratu All lmrana, aya ta: 161)*

A Hadisi, Ma'aiki (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya nuna cewa, duk wanda ya zo ranar al Ƙiyama da dukiyar gwamnati a rataye a wuyansa, to kada ma ya kusanto shi. Domin ba-shi, ba-shi[2]

Kuma yana da kyau mu sani cewa, akwai wasu hanyoyi na zalunci a Najeniya waɗanda suke halattattu a dokar ƙasa

amma a Musulunci Misali: Maƙuɗan kuɗaɗen da 'yan majalisun tarayya da na jihohi suke yanka wa kansu da sunan albashi ko alawans. Haka nan abin da ake yanka wa gwamnoni da mataimakansu, wanda ya wuce ma aunin hankali da adalci, bayan sun bar aiki. Waɗannan duka, da ire- irensu haramun ne a Musulunci. Domin a Musulunci duk abin da za a yi sai an ɗora shi a kan ma'aunin adalci.

**Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:**

" (Allah) Ya ɗaukaka sama, ya Sanya ma auni. Domin kada ku yi fin ƙarfi a ma auni. Ku tsayar da ma'auni da adalci, kada ku tauye ma 'auni (Suratur Rahman, aya ta: 7-9).

Allah yana gaya mana cewa, ya ɗaukaka sama ya sanya ma auni, watau ya daidaita ta (nauyinta bai sa) ta faɗo a kan ƙasa ba. Don haka kada ku yi fin ƙarfi a ma'auni. Watau ku ƙara shi, idan za ku auna wa kawunanku. Ku rage shi idan za ku auna wa wasu.

A nan ba ma'aunin kwano da na sikeli da na yadi da ma'unin ƙasa kaɗai, ake nufi ba. Wan nan ya haɗa ma'unin mu'amalolin jama' a gaba ɗaya. Watau a tsakanin shugabanni da talkawa ya zamo akwai ma'aunin adalci. A tsakanin masu kuɗi da matalauta ya zamo akwai ma'aunin adalci. A tsakanin mai gida da iyalinsa ya zamo akwai ma'unin adalci. Haka nan tsakanin mai saye da mai sayarwa, da mai yin aiki da mai bayar da aiki, da sauransu.

**Wannan ne ya sa Allah ya ce:**

Watau "ya sanya ma auni domin kada ku yi fin ƙarfi a yayin tsakaninku da juna Wan nan yana nuna mana cewa ma aunin adalcin da Allah ya sa a tsakanin sama da ƙasa ('gravislider), shi ya sa saman ba ta faɗo a kan ƙasa ba. Don haka idan ba mu yi adalci a harkokinmu na rayuwa ba rayuwarmu za ta hargitse ko ma ta ruguje baki ɗaya. Mu rasa yadda za mu daidaita ta. Shi kuwa adalcin ba wani ba ne illa bin tsarin Allah (Subahanahu Wata'ala).

Halin da muke ciki a Najeriya na satar mutane da kashe-kashe da tashinhankula iri-iri, a wannan zamani na damakwaraɗiyya, ya isa ya ja hankalinmu mu, mu dawo kan hanya.

7. **Jam'iyyar Da Ta Yi Nasara Tana Komawa Kamar Sarautar gado:** (Winning Party beconmes the Monarchy)

Wannan yana nuna cewa an koma a gidan jiya, wadda masu ƙago damakwaraɗiyyar suka guda tun asali Watau tsarin mulukiya na dindindin Akwai wani Karin Magana da ake cewa an ƙi cin biri an ci dila.

8. **Tana Fifita Yawa A Kan Hankali Da Nagarta**: (Majority is right )

Sanin kowa ne cewa, rinjaye a tsarin damakwaraɗiyya yana ga tarin jama'a Duk inda jama'a suka fi yawa to su suke da rinjaye.

Amma ya wajaba Musulunci yawa ba shi ne ma'auni ba Nagarta ita ce ma'auni a Musulunci Ayoyin al - Ƙur'ani suna nuna mana cewa duk inda yawa yake da wuya a sami abin kirki.

***Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:***

"**Mafi yawan su** (su kafirai) ba sa yin imani da Allah, face suna mushrikai" (Suratu Yusufà, aya ta: 106).

***Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:***

"Gaya mu su: Ku yi tafiya a bayan ƙasa, ku duba ku ga yaya ƙarshen waɗanda suka gabace ku ya kasance, mafi ya wansu sun kasance mushrikai (Suratur Rum, aya ta: 42)

***Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:***

"**Mafi yawan mutane** ba za su yi imani ba, ko da ka yi kwaɗaayin hakan (Suratu Yusuta, aya ta: 103).

***Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:***

"Alif, Lam, Ra, Waɗan nan ayoyin littafi ne. Wan nan da aka saukar a gare ka daga ubangijinka gaskiya ne Saidai mafi yawan mutane ba za su yi ba"(Suratr Ra 'di, aya ta: 1).

***Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:***

"Haƙiƙa a cikin wan nan akwai aya. **Mafi yawan su ba za su yi imani ba"** (Suratush Shu'ara i, aya ta: 8).

***Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:***

"Haƙiƙa azaba ta tabbata a kan mafi yawansu, haƙiƙa su ba za su yi imani ba (Surat Yasim, aya ta: 7).

***Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:***

"Haƙiƙa alƙiyama za ta zo. Babu kokwanto a ciknnta. Amma mafi yawan mutane ba sa yin imani (da ita) (Suratu Gafir, aya ta: 59).

***Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:***

Idan ka biya ta mafi yawan waɗanda suke bayan ƙasa za su ɓatar da kai ga bariin tafarkin Allah. Ba sa bin komai sai zato. Kirdado Kawai suke yi" (Suratul An 'am, aya ta: 116).

***Allah (Subahanahu Wata'ala) yana cewa:***

"Kuma kaɗan ne daga cikin bayina masu godiya (Suratu Saba, aya ta: 13)Wan nan duka yana nuna cewa, yawa ba shi ne yake nuna mutane suna kan daidai ba. Bin tsarin Allah shi yake nuna daidai.

**Damakwaraɗiyya A Tsakanin Dabbobi:**

Wannan hoton da kake gani a ƙasa, kuraye ne guda biyu da dan tinkiya tsakiya, za a jefa ƙuri'a a kan zaɓar wanda za a yi kalacin dare da shi. Ai kai ma ka san ba sai an fada ba. ɗan tinkiya shi ne amsa. Koda kuwa yana da yawa. Balle an fi shi yawa. To haka damakwaraɗiyya take ko ga 'yan adam Talakan nan dai shi ne a ƙasa




9. **Tana Sa Karkata ga ayyukan raya Ƙasa:** (Public infrastructure) kamar su:

Gina hanyoyi, wutar lantarki, ruwan sha, hanyoyin sadarwa, gina makarantu da sauransu.

Maimakon tun daga farko, a fara da gyara shi ɗan'adam ɗin, wajen kyautata alaƙarsa da Ubangijinsa (tarbiyyar aƙidarsa), kyautata alaƙarsa da jamaa (kyan dabi'arsa da halayensa), Inganta ƙwaƙwalwarsa (ba shi 1limi na tsoron Allah mai nagarta), wanda zai amfane shi duniya da lahira.

Ba wai muna cewa Musulunci ba ruwansa da ayyukan raya ƙasa ba ne kwata-kwata. Abin da muke cewa shi ne, a tsarin gwamnati ta Musulunci, shugaba kowanne iri ne, lallai ya fara kula da shi ɗan'adam ɗin, kafin ayyukan raya ƙasa Ayyukan shugaba .na farko su ne: Gyaran aƙidar mutane. (Watau kare addininsu). Kare rayukan jama'a. Kare hankulansu (watau kada su faɗa shaye-shaye). Kare dukiyoyinsu. (watau hana sace-sace, fashi da makami, da sauransu) Da kare nasabarsu. (watau hana yaɗuwar zina da luwaɗi da maɗigo da toshe hanyoyin yaɗuwarsu. Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam)ya ce:

"Ku saurara ku ji! Kowannenku mai kiwo ne, kuma kowannenku za a tambaye shi abin da aka danƙa masa kiwo: Shugaba, wanda yake shugabantar mutane, mai kiwo ne, kuma za a tambaye shi abin da aka danƙa masa kiwo. Mutum mai kiwo ne na mutanen gidansa, za a tambaye shi game da abin da aka danƙa masa kiwo. Mace mai kiwo ce a gidan mijinta da 'ya 'yansa. Za a tambaye ta game da su. Bawa mai kiwo ne game da dukiyar ubangidansa, kuma za a tambaye shi game da ita. Ku saurara kuji! Kowannenku mai kiwo ne, kuma kowanncnku za a tambaye shi abinda aka danƙa masa kiwo (Bukhari da Muslim suka ruwaito).

Daga Hasan (al Basari) ya ce: "Ubaidullahi bin Ziyad[13] ya je duba Ma 'aƙil bin Yasar al Muzni a rashin lafiyarsa wadda ya rasu a cikinta. Sai Ma'aƙil ya ce masa: "Zan ba ka labari wanda na ji daga Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam). Idan da na san akwai ragowar rayuwa a gare ni da ba zan gaya maka ba. Na ji Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) yana cewa: "Babu wani bawa, wanda Allah zai ba shi kiwon talakawa, ya zamaa sanda zai mutu, ya mutu yana mai yi musu algus (watau bai shiryar da su ga abinda shi ne alheri a gare su ba, ya kuma kawar da su ga barin sharri), face Allah ya haramta masa aljanna'(Bukhari da Muslim suka ruwaito).

10. **Tana Ɗaukar Mutane Kowa Da Kowa Ɗaya. Babu Wanda Ya Fi Wani.** (All people are Equal & Same)

A musulunci, Allah ya ce masu ɗa'a a gare shi (watau Musulmi), su ne masu daraja a gare shi. Haka kuma waɗanda Suke da ilimin saninsa da biyayya a gare Shi daga cikin Musulmin suna da ƙarin daraja a kan sauran, inda (Subahanahu Wata'ala) yake cewa:

"Yanzu ma sanya Musulmi da fajirai su zama ɗâya? Me ya same ku? Wane irin hukunci kuke yi?" (Suratul Ƙalam, aya ta: 35-36).

**Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce:**

"Shin za mu sanya waɗanda suka yi imani suka yi aiki na gari su zama kamar masu ɓarna a bayan ƙasa. Ko za mu sanya masu taƙawa su zama daidai da fajirai? (Suratu Saad, aya ta: 28).

**Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce:**

"Gaya musu, shin masu ilimi sa yi daidai da marasa ilimi? Masu hankali ne kaɗai, suke gargaɗuwa" (Suratuz Zumur, aya ta: 9).

Wannan yana nuna cewa, a tsarin Musulunci mutane ba ɗaya suke ba, a wajen Allah, da ma zamantakewarsu ta duniya a tsakaninsu. Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce:

"Kuma shi ne ya sanya ku masu maye wa juna a bayan ƙasa, kuma ya ɗaukaka wasunku a kan wasu, darajoji. Domin ya jarrabe ku cikin abin da ya ba Ku" (Suratul An 'ami, aya ta:165).

**Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce:**

"Muna ɗaga wanda muka ga dama, darajoji. Kuma a sama da kowane masani akwai wani masanin (Suratu Yusufa, aya ta: 76).

**Kuma Allah (Subahanahu Wata'ala) ya ce:**

Shin su ne suke raba arzikin Ubangijinka. Mu ne muka raba arzikinsu tsakaninsu a rau war duniya. Kuma muka ɗaukaka wasunsu a kan wasu, darajoji, domin wasunsu su riƙi wasu ababan horewa" (Suratuz Zukhrufi, aya ta 32).

11. **Yin Amfani Da Tasirin Kafofin Yaɗa Labarai:** (Influence of the Media)

A tsarin damakwaraɗiyya kafofin yaɗa labarai suna da tasiri matuƙa, wajen ɓata abu ko gyara shi. Idan ɗan takara yana da kuɗi, yana iya biyan kuɗaɗe masu yawa, kafafen yaɗa labarai su yi ta koɗa shi, suna ƙawata shi ga jama'a. Ta wan nan hanyar sai ya kayar da wanda ba shi da kuɗi, komai nagartarsa.

12. **Biyan Wasu Kuɗaɗe Kafin Zama Ɗan Takara:** (Money required for Candidature)

A tsarin damakwaraɗiyya kowane ɗan takara sai ya biya wasu kuɗi na tsayawa takara, (A Najeriya sun sa masa suna: Na gani ina so). Gwargwadon girman muƙamin da ɗan takara zai tsaya, gwagwadon yawan

kuɗin da zai bayar. Na shugaban ƙasa ya fi na gwamna yawa, Na gwamna ya fi na shugaban ƙaramar hukuma. Na ƙasan su, shi ne na kansula.

Tun daga nan, Zamu gane Cewa, shugabanci a tsarin damakwaraɗiyya sai mai kuɗi. Kokuma wanda masu kuɗi suka tsaya masa. Wan nan ya nuna cewa damakwaraɗiyya tsari ne na Yahudu Domin wannan shi ne abin da Banu Isra ila suka faɗa a sanda Allah ya naɗa Musu Ɗaaluta ya zama sarki a tsakaninsu:

“Suka ce, ta yaya zai kasance yana mulki a kan mu, alhali mu muka fishi cancanta da mulki, kuma ba a ba shi yawan dukiya ba?" (Suratul Baƙarah, aya ta: 247)

Wannan fa ba a nan ta tsaya ba, dole ɗan takara ya tanaji kuɗaɗen da zai bai wa masu jcfa ƙuri'a da masu yi masa farfaganda. Ka ga ke nan tun daga alwala sallar ta riga ta ɓaci.

13. **Ɓarnar Kuɗin Jama'a** (Wasteful spending).

Daga cikin illolin wan nan tsarin akwai ɓarnar dukiyar ƙasa. Duk sanda shekara huɗu ta cika za a rushe wan nan gwamnatin, a kafa wata, komai adalcinta. Haka kuma a duk inda aka sami matsala za a sake yin zaɓe a cikin waɗan nan shekarun. Haka za a yi ta kashe kuɗaɗen jama'a, maimakon ma a ce an yi musu ayyukan raya kasa (kamar yadda suke cewa).

Mu sani cewa a tsarin Musulunci, mutum shi a kan kansa, haramun ne ya ɓarnatar da dukiyarsa balle dukiyar jama' a. Wan nan shi ake kira 'almubazzaranci (ɓarnar dukiya).

**Allah (Subahanahu Wata’ala) ya ce:**

“Kuma ka bai wa makusanci haƙƙinsa da miskini da ɗan hanya. Kada ka yi almubazzaranci. Haƙiƙa masu yin almubazzaranci sun kasance yan uwan Sheɗan. Shi kuwa Sheɗan ya Kasanci mai kafirce wa ubangijinsa ne (Suratul Is 'ra'i, aya ta: 26-27).

To ina kuma ma a ce dukiyar ta jama'a ce, ba wadda mutum ya nema ya samu ta kyakkyawar hanya ba?.

14. **Kashi Saba'in Cikin Ɗari Na Yan Najeriya Ba Sa Yin Zaɓe:**

Wani abin da yake nuna cewa talakawan Najeriya sun gaji da damakwaraɗiyya (saboda illolinta) shi ne, tun daga zaɓen shekarar 2003, yawan masu jefa ƙuri'a raguwa yake yi.

Misali: A cikin yawan 'yan Najeriya kimanin miliyan ɗari biyu (200,000,000) mutum miliyan tamanin da biyar ne suka yi rijista a zaɓen shekarar 2019. A cikin wan nan adadin sai ga shi mutum miliyan goma sha biyar da dubu ɗari biyu (15,200,000) ne suka jefa ƙuri'a a zaɓen shugaban ƙasa.

Idan muka duba masu fitowa zaɓe a ƙiyasunsu cikin ɗari a shekarun mulkin damakwaraɗiyya a Najeriya, za mu gan su kamar haka:

A shekarar 2011 kashi hamsin da huɗu (54%) cikin ɗari ne suka fito jefa ƙuri'a.

A shekarar 2015 kashi arba' in da huɗu (44%) ne suka fito.

Sai ga shi a shekarar 2019 kashi talatin da biyar (35%) ne kaɗai suka fito[14].

Wannan ya nuna ɓaro-ɓaro, irin yadda yan Najeriya suke ƙin damakwaraɗiyya, amma ina! Sai daɗa ƙoƙarin ƙaƙaba musu ita ake yi.

**15. Zaɓe Yakan Nuna Jam'iyyar Da Ta Fi Yawan Kuri'u, Amma Mafi Yawan Jama'a Ba Sa Son Ta:**

Wan nan ma wata illa ce a cikin damakwaraɗiyya, wadda take nuna cewa waɗanda suka shirya wan nan tsarin sun wautar da hankulan mutane.

Yadda lamarin yake shi ne, misali: Idan aka sami jam iyyu uku a cikin ƙasa, sai jam'iyya A ta sami ƙuri' a kashi arba' in cikin ɗari (40%), jam iyya B ba ta sami kashi talatin cikin ɗari (30%), jam'iyya C ita ma ta sami kashi talatin cikin ɗari (30%), a nan sai kawai a ce jam'iyya A, ita ta cinye zaɓe. Alhali abin da zaɓen ya nuna shi ne, kashi sittin cikin ɗari (60%) na waɗanda ma suka kaɗa ƙuri'a, ba sa ƙaunar ita jam iyya A ɗin, wadda aka ce ita ce ta ci.

Ka ga a nan, ita kanta maganar bin ra'ayin mafi rinjaye (watau agalabiyya), an ajiye shi waje ɗaya, saboda tsabar wautar da hankalin jama'a.

**16. Tana Sawa A Ci Zaɓe Da Ƙasa Da Kashi Hamsin Cikin Dari Na Kuri' un Da Aka kaɗa.**

Wannan ma wani raina hankalin ne wanda yake cikin wan nan tsarin. Misali: Idan aka sami jam iyyu huɗu sun tsaya zaɓe, sai jam'iyya A ta sami kashi talatin (30%) cikin ɗari, jam' iyya B ta sami kashi ashirin (20%) cikin ɗari, jam'iyya C ta sami kashi ashirin (20%) cikin ɗari. Ita ma jam iyya D ta sami kasha ashirin (20%) cikin ɗari, sai jam'iyya A ta ci zaɓe. Kuma ka ga talatin ta samu cikin ɗari. Kai ko da ma a ce arba'in da biyar ta samu cikin ɗari, ai ba su kai rabi ba. Kuma dai har yau za mu ga bai kamata a ce fiye da rabin masu jefa ƙuri'a sun nuna ƙin su ga wannan jam'iyyar, amma sai a ce ita ce ta ci zaɓe. Ba wai muna cewa wan nan haka yake a ko 'ina ba, amma dai ana yi.

**17. Tana Sawa A Zaɓi Shugaba Domin Ya Bayar Da Cin Hanci**:

Haramun ne a Musulunci ka zaɓi mutum domin ya ba ka abin duniya, ko domin ya yi alƙawarin zai ba ka.

*Daga abu Hurairah (Radiyallahu Anhu) ya ce:*

*Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Mutum uku, Allah ba zai yi Magana da su ba ranar alƙiyama. Ba zai kalle su ba. Kuma ba zai tsarkake su ba. Kuma azaba mai raɗaɗi ta tabbata a gare su: Mutumin da ya hana ɗan hanya rowan da, shi ya riga ya gama tasa buƙatar da shi. Da mutumin da ya sayar wa da wani abin sayarwa bayan La'asar, yana mai yi masa rantsuwa da Allah, cewa shi ma kan kaza da kaza take a wajensa, ya gasgata shi, alhali ba hakan ba ne. Da mutumin daya goyi bayan shugaba, bai goyi bayansa ba sai kawai domin zai bashi abin duniya. Idan ya bashi, sai ya cika masa alƙawarin (daya yi masa). Idan kuwa bai bashi ba, ba zai cika masa wannan alƙawari ba" (Bukhari da Muslim Suka ruwaito).*

**18. Tana Samar Da Shugabanni Maƙaryata:**

Kasancewar shi tsarin damakwaraɗiyya an ɗora shi ne a kan cewa, shugabanni za su yi wa talakawa alƙawuran abin da za su yi musu a lokacin neman zaɓe; wan nan yana sanya shugabanni su rinƙa yin alƙawuran ƙarya.

Mun dai faɗa a baya cewa, a tsarin siyasar Musulunci alƙawarin da Shugaba zai yi wa talakawa shi ne, tafiyar da su a kan tsarin Al-Ƙur'ani da Sunnah.Su kuma sun yarda cewa tsarin Allah zai ba su duk wani jin daɗi, na duniya da lahira.

Mu sani cewa a Musulunci, ƙarya tana daga cikin kaba'irai, (watau babban zunubi ce). Duk wanda aka san shi da ita bai ma halatta ya zama shugaba ba.

*Daga Abu Hurairah (Radiyallahu Anhu) ya ce:*

*Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Mutum uku Allah ba zai yi magana da su ba ranar al ƙiyama. Ba zai tsarkake su ba. Ba zai kalle su ba. Kuma azaba mai raɗaɗi ta tabbata a gare su: Tsoho mazinaci da shugaba maƙaryaci da matalauci mai girman kai" (Muslim ne ya ruwaito).*

**19. Mace Za Ta Iya Zama Shugaba:**

Malaman Musulunci gaba ɗaya sun haɗu a kan rashin halaccin shugabancin mace. Saboda Hadisin Abu Bakrata, wanda ya rawaito kamar haka:

"Yayin da labari ya isa ga Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) cewa, mutanen Farisa sun shugabantar da 'yar Kisira (watau 'yar shugabansu), sai ya ce: "Duk mutanen da suka shugabantar da mace a lamarinsu ba za su rabauta ba (Bukhari ne ya ruwaito).

Mu sani fa cewa addinin Musulunci shine ya ƙwato 'ya mace daga ƙangin wulaƙancin da ta sha a tsakanin al'umomin Girkawa da Farisawa da Larabawa da sauransu, da ƙyamar da addinin Yahudanci da na Kiristanci suka yi mata. A addinin Yahudanci an samu suna ƙyamar mace idan tana haila. Akan nisanta ta da mutane. Koda mazubin da ta ci abin ba a taɓawa. A tsarin Kiristanci kuwa, a da, ba su yarda mace tana da rai ba, sai bayan wani lokaci aka ƙwato mata wan nan 'yancin.

Wajibi ne mata musulmi da ƙungiyoyin mata su karanta Tarihin 'ya mace a waɗan can al'umomi da waɗan nan addinai. Wan nan zai sa mu gane cewa Musulunci ba wulaƙanta 'ya mace ya yi ba, da ya hana taa shugabanci da alƙalanci.

Abin da ya sa Musulunci ya hana 'ya mace waɗannan ayyuka shi ne, ayyuka ne na gwamutsi da maza. Sannan kuma yanayin halittarta, kasancewa Allah ya ƙaddara mata yin haila duk wata, da daukar ciki da shayarwa da raino; Waɗan nan ayyukan da Allah ya ɗora mata abin dubawa ne. Don haka a sakc ɗora mata waɗan can manyan ayyuka na Jama'a akwai cutarwa. Sai a yi biyu babu. Sannan kuma ai kasancewar shugabanmu Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ƙyamaci abu, ya kamata mu ƙyamace shi, matuƙar mun yarda shi shugabanmu ne, kuma Manzan Allah ne.

**20. Tana Sawa A Naɗa Mutane A Muƙaman Da Ba Su Da Ƙwarewa A Kai. Sai Saboda Biyan Buƙatar Siyasa.**

Musulunci bai yarda a naɗa mutum a wani muƙami na gwamnati ba, sai mai amana da ƙwarewa a wan nan fagen. Al-ƙur ani ne ya koyar da mu haka a Suratu Yusufa da Suratul Ƙasas.

**A Suratu Yusufa al-ƙur' ani yana gaya mana abinda Annabi Yusufa (Alaihissalam) ya ce wa sarkin Masar:**

"Ya ce "Sanya ni a (ɓangaren kula da) taskokin ƙasa. Ni mai kula da amana ne, kuma mai ilimi ne (a wan nan ɓangaren)" (Suratu Yusufa, aya ta: 55)

A suratul ƙasas kumaʻyar annabi Shu'aibu ce take shawartar mahaifinta, ya ɗauki Annabi Musa aiki, sabo da suffofin da ta lura da su a tattare da shi. Inda take cewa:

"Ya babana ka ɗauke shi aiki. Mafificin wanda za ka ɗauka aiki, shi ne ƙaƙƙarfa, mai amana (Suratul Kasas, aya ta: 26.)

Wan nan ya nuna mana cewa, duk aikin da za a ɗauki mutum, bayan amana, dole Sai ya zama yana da ƙwarewa a wannan fagen, ƙwarewa ta ilimi ko ta ƙarfi.

Wani abin da ya fi ban tsoro shi ne, Hadisin da aka ruwaito daga Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) game da naɗa mutum a wani ofishi, domin biyan buƙata ta son rai.

***“An ruwaito daga Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce:***

"Wanda duk ya shugabanci wani abu na Musulmi, (kamar a ce, ya zama Shugaban ƙasa, ko ya zama gwamna ko shugaban ƙaramar hukuma ko sarki), sai ya naɗa mutum, alhali ya sami wanda ya fi shi nagarta ga Musulmi, to ya ha 'inci Allah da Manzonsa. A wata ruwayar,

"Wanda duk ya rataya ragamar wani aiki ga wani mutum a wata jama 'a, alhali a cikin wan nan jama ar ya sami wanda ya fi soyuwa a wajen Allah, to haƙiƙa ya ha inci Allah. Ya ha 'inci Manzonsa. Ya ha’inchi Muminai” (Hakim ne ya ruwaito).

Idan muka duba sai mu ga a ita tsarin damakwaraɗiyya galibi jam'iyya ake dubawa ko wani kusanci na son zuciya. Ba a cika duba nagarta ba.

21. **Tana Janyo Rashin Ɗorewar Ayyuka Da Tsare-Tsare.**

Babu shakka sanin kowa ne cewa, mu dai a Najeriya, komai kyan tsarin da wani Shugaba ko gwamna ya zo da shi, kuma komai amfaninsa, idan bai yi wa magajinsa daidai ba, sai kawai ya dakatar da shi, ko ma ya rushe shi.

A nan za mu ga cewa, hatta ita kanta damakwaraɗiyyar ana saɓa mata. Domin da kamata ya yi a lura da amfanin aikin ga mutane ko rashin amfaninsa.

To dai a taƙaice Musulunci bai yarda da ɓarnar dukiya ba, koda kuwa ta mutum ce, balle dukiyar jama'a. Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) yana cewa:

"Haƙiƙa Allah ba ya son abu uku a gare ku: "Wane ya ce, wane ya ce. Da lalata dukiya. Da yawan roƙo (Bukhari da Muslim suka ruwaito).

**NASIHA GA 'YAN UWA MUSULMI:**

A ƙarshe nasihata ga yan' uwana Musulmi ita ce, shi wan nan tsari naa damakwaɗiyya, asalinsa ba na Musulmi ba ne, kamar yadda muka karanta a sanda muke bayanin asalinsa. Don haka sai mu duba, mu ga abin da za mu kauce wa a zukatanmu (watau kada mu yarda mu ƙudure shi a zuci), da abin da za mu ƙaurace wa aikace. Sai kuma mu shiga tunanin yadda wata rana za mu maye siyasar musulunci a maimakonsa.

Amma fa ni na san ko bayan rammu, wata rana su da kansu waɗanda suka ɗora mu a kan wannan tsarin za su bar shi su kawo mana wani tsari daban. Sai mu lura, ma san kammu.

Amma mu sani cewa an tambayi malaman zaunannen kwamatin bayar da fatawa (na Saudiyya): Shin ya halatta jefa ƙuri'a ko a shiga zaɓe a ƙasar da take aiki da saɓanin abin da Allah ya saukar. Ga yadda amsar ta zo:

“Ba ya halatta ga Musulmi ya tsaya takara domin ya saka kansa cikin gwamnatin da take hukunci da saɓanin abin da Allah ya saukar, take aiki da saɓanin shari'ar Musulunci. Ba ya halatta ga Musulmi ya zaɓe shi, ko ya zaɓi wani, daga cikin waɗanda za su yi aiki a wan nan gwamnatin. Saidai idan shi wanda zai tsaya takarar, da waɗanda za su zaɓe shi suna ƙaunar shiga ne domin su kai ga canza hukunci zuwa ga shari'ar Musulunci. Kuma suka ɗauki wan nan ta zama hanya ga samun rinjaye a tsari gwamnatin. Da sharaɗin shi wanda zai tsaya ɗin, ba zai yi aiki ba, bayan ya shiga, sai a wuraren da ba su saɓa da shari'ar Musulunci ba”

**KAMMALAWA**

Godiya ta tabbata ga Allah (Subahanahu Wata’ala). wanda ya shiryar da ni, ya ba ni ikon kammala rubutun wannan littafi a yau Alhamis 1 ga Watan muharram, shekarar hijjra 1442, wanda ya yi daidai da 20 ga watan Agusta, shekerar miladiyya 2020.

A wannan littafi, na kawo bayanai game da ita kanta siyasa da kuma ita damakwaraɗiyyar. Sai kuma na jero illolin wannan tsari nan damakwaraɗiyya da muke ciki, domin wayar da kan jama'a, musamman yan'uwa Musulmi, su gane cewa abin da ya sa muke ta kuka da damakwaraɗiyya shi ne saɓa wa tsarin Allah da ta yi, illa iyaka.

A ƙarshe, ina roƙon Allah (Subahanahu Wata’ala) ya sa ɗan wan nan aiki da na gabatar ya zamo mai amfani ga Musulmi. Ya zamo ta hanyarsa mun fahimci illolin da suke cikin wan nan tsari na damakwaraɗiyya. Mu zama muna shirin kauce masa, gwargwadon iko. Muna ƙoƙarn ɗabbaƙa siyasar Musulunci. Allah ya sa haka, amin.

**Dr Yahaya Tanko**

Babban Limamin Masallacin Umar Bin Khaɗɗab Gyaɗi-gyaɗi Kano. Kuma Malami a Jami'ar Yusufu Maitama Sule dake Kano (a yanzu).

08060846703

tankoyahaya007@gmail.com